## ABOUT CITAD

CITAD (www.citad.org) is a capacity building Civil Society Organization whose activities covers Research, Advocacy, Training and Publicity in all areas of ICTs.
Its vision is; a Knowledge-based Democratic Society free of Hunger while its Mission is; Using ICTs to Empower Citizens for a just and knowledge-based Society that is anchored on sustainable and balanced development.


## MAIN OFFICE:


3rd Floor, NISTF Building, No.1A, Social Insurance Road, Behind Trade Fair Complex, Zaria Road, Kano. P.O. Box 10210, Kano, Nigeria.
GSM: 0800-68078282, 080-54362931, 070-33427467
• E-mail: info@citad.org, Citadev@gmail.com, citad4peace@citad.org, Website: www.citad.org, www.citad4peace.org.ng

## BAUCHI OFFICE:

NUJ Secretariat, Opposite Reinsurance House, Ahmadu Bello Way, Bauchi State.
GSM: 08064867312


CITAD actionaid UKaid from the British people

# KUNDIN SAMAR DA TSARIN CI GABAN CIKIN GARIN RANO



*Tsarawar*

**Cibiyar Bunƙasa Fasahar Sadarwa Da Ci Gaban Al'umma (CITAD)
Tare Da
Gudummawar Ƙungiyar ActionAid Ta Najeriya (AAN)**

CITAD

*A Knowledge-Based Democratic Society Free of Hunger*

# ABUBUWAN DA KE CIKI


Jadawali....i

Godiya....ii

Gabatarwa....1

Manufa....2

Tsarin da aka yi amfani da shi....5

Taswirar Garin Zinyau....6

Yanayin Zamantakewa....9

Harkar Lafiya....10

Ilimi....10

Juyawar Yanayi....12

Kadarori....13

Tantance Haɗɗura....13

Tantance Haƙƙoƙin Mata....14-18

Teburin Lissafin Haƙƙin Mata....19

Kalubale....20

Tantance Matsaloli Ta Amfani Da Bishiyar Matsaloli....23-24

Waɗanda zasu iya Tallafawa....26

Cibiyoyi....26

Tantance Yanayin Karfin iko....26

Tantance Hanyoyin samun bayanai....29

Tsarin da Za abi....30

# GODIYA

Wallafawar wannan littafi yasamu yiwuwane tareda tallafi daga Sashin Kula da Cigaba na ƙasa da ƙasa na Gwamnatin Birtaniyya (DFID ta hannun ƙungiyar ActionAid Nigeria (AAN). Dole ne a yabawa wannan Cibiya ta ActionAid saboda jajircewa ta wajen Bunƙasa Demokuraɗiyya ta hanyar wayar da Jama'a su fahimci Demokuraɗiya.

Muna godiya ta musamman ga Shugaban Cibiyar Fasahar Sadarwa da Ci gaban Al'umma (CITAD), Y.Z. Ya'u domin kasancewarsa jigo wanda ya bada gudummawa ga kammaluwar wannan Littafi.

Godiyar mu bazata cikaba sai mun yaba da Kyakkyawar fahimta da hadin kai da ma'aikatan CITAD. Haka kuma mun yabawa da ƙoƙari da himmar Malam Ahmad AbdullahiYakasai, da Isyaku Garba' da Abubakar Auyo da Mukhtar Sulaiman Umar da Abdullahi Jido da Harira Abdulrahman wanda suka hana kansu hutu domin tabbatar da kammaluwar wannan Kundi.

Muna miƙa cikakkiyar godiyarmu ga 'Yan kwamitin aiwatar da kundin wannan Gari na Rano ta Tsakiya da Mai Gari da Dagaci da kuma dukkannin waɗan da suka tallafa wajen gudanar da tsarin shirin wannan kundi, babu shakka zai ingan ta shirin nan gaba.





# GABATARWA

Wannan kundi na cigaban wannan gari yana ɗauke da gaba ɗayan bayanai filla-filla da kuma taƙaitattun abubuwan da suka shafi garin Rano da ke ƙaramar hukumar Rano a jihar Kano a tarayyar Najeriya. Wannan kundi zai zama wata madogara na yin izna wajen tabbatar da gaskiyar al'amura ga jama'ar Garin Rano. Kundin yayi cikakken bayanin garin da mutanensa da kuma albarkatun ƙasa da Allah Ya hore masa. An tattaro waɗannan bayanai ne daga wajen wasu keɓantattun mutane mazauna garin ta hanyar yin amfani da tsarin waiwaye adon tafiya domin yin bitar abubuwan da suka gudana da kuma tsarin nan na Action Aid wanda ke baiwa kowa damar bayar da gudummawa don tattarawa da faɗakar da mutane sanin muhimmancin kowa ya shiga a dama da shi a al'amuran zaɓe wanda aka fi sani da (SCEEP).

Tsarin zai zama wani ginshiƙi na aiki tare da wasu garuruwa a ƙoƙarin saita al'umma kan gwadaben da za su rinƙa bibiyar abubuwan da gwamnatoci da wakilansu ke gudanarwa. Haka kuma, wannan kundin zai samar da wata kafa ta yin aiki tare tsakanin al'ummar gari da waɗanda suka zaɓa zuwa matakai daban-daban. An samar da kundin ne ta bin managartan tsare-tsare da wannan ƙungiya ta yi a baya, aka tattaro ƙwararru suka yi aiki ƙarƙashin inuwa ɗaya.

Hanyar amfani da tsarin waiwaye adon tafiya na yin amfani da cikakken bincike kamar binciko dangantakar mahukunta da haƙƙoƙin al'umma musamman mata da gano abubuwan da ke yi wa garin barazana da binciko ƙungiyoyi da mutanen da za su iya tallafawa da fahimtar hanyoyin sadarwa da al'ummar garin ke amfani da su da kuma matsalolin da suke ci musu tuwo a ƙwarya.

Domin cimma nasara abubuwan da aka ambata a sama, ActionAid ta aiwatar da tsarin waiwaye adon tafiya a garin ta amfani da sassa bakwai na tsarin tantancewar bayanai. Bayanan da aka tattara za su zama ginshiƙi na ƙarfafa gwiwa wanda zai ciyar da garin gaba yadda ake buƙata.

## MANUFA

Manyan manufofin wannan kundi su ne kamar haka:

- Gano tare da a dana al'amuran da suka shafi cikin garin Rano tare da fitar da wani tsari na shigo da al'ummar yankin don yin aiki tare.
- Zaburar da al'umma wajen neman abubuwan ci gaban garin daga wakilansu a ɓangarori daban-daban.
- Tallata ƙwarewa da ilimi da kuma abubuwa da cikin garin Rano ke fatan samu a dunƙule domin samun sauƙin bibiya.

## HANYOYIN DA AKA YI AMFANI DA SU

Hanyoyin da aka bi wajen aiwatar da aikin sun haɗa da:

- Tattaunawa tun a karon fari tsakanin dattawan cikin garin Rano da CITAD.
- Ziyarce-Ziyarce: An ziyarci wurare daban-daban tare da ganawa da mutanen na garin na tsawon kwanaki domin samun cikakkun bayanai na ɓangarori bakwai na wai waye adon tafiya (Reflection Action).
- Taron tantancewa da rubuta rahoton abubuwan da aka gano.

## TSARIN DA AKA YI AMFANI DA SHI

- An yi amfani da abubuwa daban-daban wajen tantance ɓangarori bakwai na wai waye adon tafiya (Reflection Action).
- An yi amfani da taswira wajen binciko matsalolin da ke addabar garin.
- An yi amfani da jerin gwanon haƙƙoƙi ɗan'adam wajen gano haƙƙoƙin al'ummar cikin garin Rano.
- Jera abubuwa mafi sauƙi ya taimaka wajen tsara al'amuran da suka fi muhimmanci bi da bi waɗanda al'ummar garin suka gano.





- An yi amfani da bishiyar-matsaloli domin fahimtar abubuwan da suka haddasa matsalolin da tasirinsu da kuma tattaunawa mai zurfi a kansu.
- An yi amfani da salon tantance cibiyoyi da mutanen da za su iya bayar da tallafi domin gano waɗanda za su iya hoɓɓasa kuma suke da ikon kawo canji ga abubuwan da garin ke buƙata.
- An yi amfani da tsarin zane na Venn domin a tantance matakin tasirin da cibiyoyi da mutanen da za su iya taimakawa da alaƙarsu da garin.
- An yi amfani da salon akasa a fai-fai wajen tantance haƙƙin mata.
- Tsarin tantance matsaloli ya fitar da abubuwa daban-daban da ka iya cutar da garin.

Zanen hanyoyin sadarwa ya tantance hanyoyin da al'ummar garin ke isar da saƙo tsakaninsu da sauran garuruwa da waɗanda za su iya bayar da gudummawa. A ƙoƙarin aiwatar da tantance abubuwa daban-daban, an tattauna da kowa da kowa, an tattauna a ƙungiyance don a yi tambayoyi da kuma yin bincike mai zurfi domin a samu tantancewa mai inganci.

CIKAKKEN BAYANI GAME DA CIKIN GARIN RANO

Sunan Gari: Cikin Garin Rano
Karamar Hukuma: Rano
Jiha: Kano
Adadin Al'umma: 14,544 (Abisa ƙiyasi Maza 7,497, Mata 7,047)

## AJUJUWAN SHEKARUN AL'UMMAR CIKIN GARIN RANO

| | |
|---|---|
| Shekara 0 zuwa 5: | 2,099 |
| Shekara 6 zuwa 10: | 2,440 |
| Shekara 11 zuwa 18: | 2,890 |
| Shekara 19 zuwa 30: | 2,326 |
| Shekara 31 zuwa 40: | 1,873 |
| Shekara 41 zuwa 50: | 1,236 |
| Shekara 51 zuwa 60: | 1,091 |
| Shekara 61 zuwa 70: | 409 |
| Shekara 70 zuwa Sama: | 180 |
| Adadi | 14,544 |

Aikin yi: Noma, Ma'aikatan Gwamnati manya da ƙananan 'Yan Kasuwa

Kayayyakin da aka fi sayarwa: Kayayyakin masarufi, kayayyakin abinci da sauran kayayyakin sayarwa na yau da kullum.

Kuɗaɗen da ke shigowa/Kuɗaɗen da ake kashewa
Matsakaicin abin da ke shigowa mutum a shekara: ₦292, 000
Matsakaicin abin da mutum yake kashewa a shekara: ₦401, 000
Matsakaicin abin da ma'aikaci yake samu a kullum: ₦444, 000
Matsakaicin abin da ma'aikaci yake kashewa a shekara: ₦540, 000

## HARKAR LAFIYA

Babban asibitin wannan ƙaramar hukuma ta Rano na cikin wannan gari wanda nisan sa ke ƙasa da kilo mita ɗaya. Akwai ƙwararrun ma'aikatan lafiya guda 33, maza 22 mata 11 da ke kasan cewa kodayaushe a asibitin kuma suna da kyakkyawar ma'amala wajen kula da maras lafiya yayin ɓarkewar wata annoba. Kason mutanen da suka fi gamuwa annoba sune yara 'yan ƙasa da shekar biyar. Mafi yawancin haihuwa ana karɓar tane a wannan asibiti, bugu da ƙari akwai ci gaba sosai a wannan asibiti shekaru uku baya da suka shige.






## ILIMI

Makarantu: Akwai makarantun firamare 3 da na sakandare 4 cikin a garin Rano waɗanda nisansu bai wuce tafiyar mita 500.

| | | | |
|---|---|---|---|
| Adadin yaran da suka shiga makaranta a halin yanzu: 835 | Adadin Yara Maza: 1,438 | Adadin Yara Mata: 1,397 | Adadin 'yan ƙasa da shekara 5: 462 |
| | Adadin yara 'yan shekaru 6 zuwa 10: 1,278 | Adadin 'yan shekaru 11 zuwa 15: 2,131 | Adadin 'yan shekaru 16 zuwa 20 (idan ana buƙata): 09 |
| Adadin waɗanda suka kammala Firamare: 13,062 | | | Adadin Maza: 8,691 |
| | | | Adadin Mata: 4,371 |
| Adadin waɗanda suka kammala Sakandare a garin: 11,690 | | | Adadin Maza: 6,720 |
| | | | Adadin Mata: 4,970 |
| Adadin waɗanda suka kammala Makarantar gaba da Sakandare: 2,488 | | | Adadin Maza: 6,720 |
| | | | Adadin Mata: 4970 |
| Adadin waɗanda ba su taɓa zuwa Makaranta ba: 5,950 | | | Adadin Maza: 2,252 |
| | | | Adadin Mata: 3,698 |
| Adadin yaran da suka daina zuwa Makarantar Firamare: 2,384 | | | Adadin Maza: 1,206 |
| | | | Adadin Mata: 1,178 |
| Adadin yaran da suka daina zuwa Makarantar Sakandare: 3,339 | | | Adadin Maza: 2,080 |
| | | | Adadin Mata: 1,259 |

Masu Buƙata ta musamman (PWDs): 74(Wannan kiyasi ne yayin tattaunawa)




## TARIHIN CIKIN GARIN RANO

Cikin garin Rano na daga cikin ƙananan hukumomi guda 44 dake jihar Kano, wannan gari nada kimnin nisan kilo mita 52 daga cikin birnin Kano. Kamar yadda manyan gari ke faɗa, Cikin Garin Rano ya samo asali ne tun wajen hijira ta 1953 daga turawan mulkin mallaka da suka yi da nufin haɓakawa da kuma ƙara birnantar tsohon garin daga tsohon tsarin birane da aka kwashe dubunnan shekaru da suka wuce ana amfani da shi.

Fitat da taswirar birnin na Rano anyi shi ne ƙarƙashin kulawar wani bature wanda akafi sani da Maigunduma ( Zonal officer ). A lokacin

an fahimci cewa mutane basu damu da su tashi daga gurinba harma dashi kansa sarkin wanda ke zaune a Kibiya ( wadda yanzu ƙaramar hukuma ce) saboda kasancewar gurin yayi daji, babu zato babu tsammani sai wani wanda akafi sani da Iro-wuya a matsayin wanda ya fara tashi daga tsohon garin ya koma sabon garin na Rano.

Wannan gari Allah ya albarkace da nau'in kasuwanci daban-daban, ma'aikatan gwamnati,da kuma 'yankasuwa kamar su Alh. Auwalu Abdullahi wanda akafi sani da A.A Rano, Alh. Danlami SALBAS da makamantasu. Kamar yadda aka sani Rano na ɗaya daga cikin gundumomi na Hausa bakwai AutanBawo a matsayin sarki. Cikin garin Rano anan ne inda gidan sarki yake kuma yana kuma ya jima yana fuskantar matsalar ruwa wanda mazauna wannan gari sai sunyi tafiya kamar ta kilomita guda kafin su sami rowan da zauyi amfani das hi. A sakamakon haka ne yasa kowane loko da saƙo sai ka sami 'yan garuwa dake sayar da ruwa akan kuɗi naira goma sha biyar ( N15:00) kowace jarka.

TASWIRAR CIKIN GARIN RANO


Matasan wannan gari su suka jagoranci fitar da taswirar wannan gari. Waɗanda suka taimaka wajen fitar da taswirar sun haɗadda matasa,mata, masu buƙata ta musamman, yara da kuma manyan gari.Wannan ya bada cikakun bayanai da kuma damammaki azahiri. An kuma gano wasu alamomi yayin fitar da wannan taswirar waɗanda suka haɗarda ma'adanai, ababan more rayuwa, da kuma aikace-aikace . Anyi wannan taswirar ne domin a gano sauye-sauyen da aka samu a wasu shekaru da suka wuce da kuma kyakkawan zaton wasu canje-canjen da ake sa rai zasu iya samuwa nan gaba. Daga cikin abubuwan da wannan taswira ta ƙunsa ya haɗar da gidaje, makarantu, babban asibiti, masallaci,Tafkin Rano, duwatsu, kasuwa da kuma guraren yin noma kowace shekara.



KUNDIN SAMAR DA TSARIN CIGABAN CIKIN GARIN RANO 2016






## YANAYIN ZAMANTAKEWA
(ABISA KIYASI MAZA, MATA)

Rano cikin gari maraya ce wanda tana da ƙiyasin yawan al'uma kimanin 14,544 (7,497 maza, 7,047 mata). Bisa ƙiyasi ƙididdiga ta nuna cewa daga cikin al'umar wannan gari an samu cewa waɗanda ke shekaru tsakanin 0-5 su suka fi yawa.

Bugu da ƙari, mutanen wannan gari mafi yawancin su sun haɗar da ma'aikatan gwamnati, masu sana'ar hannu, 'yan kasuwa da kuma manoma da ke noman kayan rafi lokacin rani da kuma sauran kayan abinci a lokacin damina waɗanda suke samun matsakaicin kuɗin shiga kimanin N 292,000 , a wani ɓangare kuma kowane magidanci bisa ƙiyasi na kashe kimanin N 401,500 a shekara. Mazauna wannan gari kusan suna kashe ɗan kuɗin da ya shigo. Akwai kuma masu sana'a ta hannu wandu suma bisa ƙiyasi suna




## HARKAR LAFIYA
A cikin garin Rano akwai babban asibiti guda ɗaya da kuma cibiyar kula da marassa lafiya. A shekarun baya da suka wuce wannan gari ya sha fama ɓarkewar annobar cututtuka kamar su kwalara,zazzaɓin cizon Sauro, tayifoyid, da kuma gudawa. Asibitin nada yalwa kuma akwai gogaggun ma'aikatan lafiya har guda 33, daga ciki akwai maza 22 yayinda ake da mata 11. Bugu da ƙari asibiti yafi kula mata kuma akwai mata unguwar zoma da aka baiwa horo domin su taimaka wajen karɓar haihuwa domin rage cunkoso. A halin yanzu anada bukatar a ƙara wasu ma'aikatan horo musammamma mata.



## ILIMI
Mafi yawancin makarantun annan sun ginu sosai kuma akwai wadattun ajujuwa da kuma filin wasa amma duk da haka waɗansu makarantun nada buƙatar gyare-gyare da kuma ƙarin ajujuwa, daka cikin irin waɗananna makarantu suna da buƙatar ruwa.






Anyi amfani da shirin bunƙasa damar samun ilimi na PRS domin auna ingancin ilimi a cikin garin Rano. Shirin bunƙasa damar samun ilimi PRS ya fayyace haƙƙoƙi guda 10 da aka samu daga dokokin ƙasa, misali anyi amfani da kundin tsarin mulkin ƙasa da tarukan kare haƙƙin ɗan Adam wajen tantance ingancin ilimi a cikin garin Rano.

Babbar manufar wannan shiri na PRS shine shigar da 'yan ƙasa cikin tsarin bunƙasa ilimi. Anyi amfani da kundin wajen tantance mizanin fahimtar damar samun ilimi musamman ta fuskar al`umar wannan yankin su san cewar damar su ce.

Yarjejeniyar bunƙasa damar samun ilimi PRS na cikin garin Rano

| S/N | Yarjejeniyar PRS | Tantancewa (1 mafi ƙaranci, 5 mafi girma) |
|---|---|---|
| 1. | Haƙƙin samun Kyakkyawan Ilimi kuma Kyauta | 3 |
| 2. | Haƙƙin rashin nuna wariya | 4 |
| 3. | Haƙƙin Samar da Isassun Kayayyakin More Rayuwa | 5 |
| 4. | Haƙƙin Samar da Wajen Zama Mara Haɗari | 4 |
| 5. | Haƙƙin Samar da Kwararrun Malamai | 4 |
| 6. | Haƙƙin Samar da Tsarin Koyarwar da ya Dace | 2 |
| 7. | Haƙƙin Sanin 'Yancin Kai | 2 |
| 8. | Haƙƙin a dama da Mutum a Wajen Ɗaukar Mataki | 1 |
| 9. | Haƙƙin Samar da makaranta mara ƙunbiya-ƙunbiya | 2 |
| 10. | Haƙƙin Samar da Ingantacciyar Koyarwa | 4 |

*Jadawali na sama na nuna mana cewa mutanen wannan gari ba'a tattaunawa dasu domin ɗaukar mataki kuma babu ingantaccen dama ta samun ilimi kyauta da kuma samar da tsarin koyarwa da ya dace ( manhaja).*



10 Core Educational Right Rano Central

| PRS Charter | Rate |
|---|---|
| 1- Right to free and fair education | 3 |
| 2- Right to non-Discrimination | 4 |
| 3- Right to Adquate Infrustructure | 5 |
| 4- Right to safe and non vollance enviromment | 4 |
| 5- Right to Quality trained teacher | 4 |
| 6- Right to relevant Curriculum | 2 |
| 7- Right to know your right | 4 |
| 8- Righ to transperent and accountable schools | 2 |
| 9- Right to participate in Decision making | 1 |
| 10- Right to Quality learning | 4 |



KUNDIN SAMAR DA TSARIN CIGABAN CIKIN GARIN RANO 2016



## JUYAWAR YANAYIN

Cikin Garin Rano na da yanayi iri biyu; rani da damina. Ana samun yanayin rani ne daga Nuwanba zuwa Afirilu.Damina kuwa tana farawa daga watan Mayu, inda ruwa yakan kankama tsakanin Agusta da Satumba. Jihar Kano kacokan ta fi samun yanayin zafi da yawa,

Ruwan sama (watau damina) yawanci akan same shi ne a watannin Mayu da Yuni da Yuli da Agusta da kuma Satumba. Kano na samun rani a watannin Janairu da Fabrairu da Agusta. Akan samu matsakaicin zafi a watan Afrilu, yayin da sanyi ya fi tsananta a watan Agusta. Satumba shi ne watan da aka fi samun ruwan sama, haka kuma Janairu ne watan da rani ya fi ƙamari. Ayyukan noma a garin yana da yawa sosai sannan kuma ga kasuwanci. Mutane a Rano suna fara shirye-shiryen shuka a tsakanin Afrilu da Mayu. Jadawalin da ke biye yana nuna yadda yanayin ya karkasu da kuma yadda ayyukan suke gudana a tsakanin waɗannan lokutan.



RANO CENTRAL SEASONAL CALENDER 08-1

| | JAN | FEB | MARCH | APRIL | MAY | JUN | JUL | AUG | SEP | OCT | NOV | DEC |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|
| Dying | L | L | L | M | M | VH | VH | L | L | H | H | L |
| 2. Taloring | L | L | L | M | M | VH | VH | L | L | H | H | L |
| 3 Capentary | L | H | L | L | L | L | L | L | H | VH | VH | VH |
| 4 Bulding | L | H | L | L | L | L | L | L | H | VH | VH | VH |
| 5. Weldering | M | M | M | M | M | M | M | M | H | H | H | H |
| 6. Farming | L | L | L | M | H | H | H | H | H | H | H | H |

# TSAWON SHEKARA

| S/N | Sana'oi da Harkoiki | Yanayi | Janairu | Fabrairu | Maris | Afrilu | Mayu | Yuni | Yuli | Agusta | Satumba | Oktoba | Nuwamba | Disamba |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|
| 1. | Rini | VL | L | L | L | M | M | VH | VH | L | L | H | H | L |
| 2. | Dinki | VL | L | L | L | M | M | V.H | V.H | L | L | H | H | L |
| 3. | Kafinta | VH | L | H | L | L | L | L | L | L | H | V.H | V.H | V.H |
| 4. | Magina | L | L | H | L | L | L | L | L | L | H | VH | VH | V.H |
| 5. | Walda | | M | M | M | M | M | M | M | M | H | H | H | H |
| 6. | Noma | | L | L | L | M | H | H | H | H | H | H | H | H |

Karin haske: VH ƙwarai da Gaske, H ƙwarai, M Matsakaici, L ƙasa, VL ƙasa Sosai

## AIKACE AIKACEN AIYUKA YAU DA KULLUM CIKIN GARIN RANO NA MAZA


| LOKACI | AKACE AIKACE |
|---|---|
| 5:00am- 7:00am | Lokacin yin salla, lokacin Karin kumallo da yin wanka |
| 7:00am 8:00am | Kai yara makaranta da kuma tafiya wajen aiki |
| 8:00- 6:00pm | Ci gaba da harkokin kasuwanci |
| 7:30pm-8:30 | Sallar magariba, jin labarai,, zuwa wajen karatuttukan addini,da kuma zuwa wajen taron unguwa. |
| 8:30- 10:00 | Sauraren nishaɗantarwa daga radio |
| 10:00pm | Lokacin barci |


## AIKACE AIKACEN AIYUKA YAU DA KULLUM CIKIN GARIN RANO NA MATA

| LOKACI | AKACE AIKACE |
|---|---|
| 5:00am- 6:00am | Lokacin yin salla, |
| 6:00-7:00am | Shirya kayan Karin kumallo, sauraren labrai, shirya yara zuwa zuwa makaranta |
| 7:30- 10:00pm | Share gida da kuma wanke-wanke |
| 10:00-12:30 | Hutawa wasu kuma sunayin 'yan kasuwancin su |
| 11:00am - 1:00 pm | Abincin rana da kuma wanke kayan yara |
| 1:00pm- 2:30pm | Lokacin sallah da ɗauko yar daga makaranta |
| 2:30pm 4:00pm | Baiwa yara abinci da kaisu makarantar Islamiyya |
| 4:00pm -6:00pm | Share gida da dafa abincin dare |
| 6:00pm- 9:00pm | Cin abincin dare kallon labarai, hira da iyali. |
| 9:00pm 10:00pm | Sauraren labarai |
| 10:00pm | Lokacin barci |









WOMEN DAILY ACTIVITY CHART

| TIME | ACTIVITIES |
| --- | --- |
| 5:00 am – 6:00 am | prayer time |
| 6:00 am – 7:30 am | listen to news, prapare Break fast Bath their children and send them to school |
| 7:30 – 10:00 am | Tidy up the st House, take their break fast, wash their Cloths. and washing of plates. |
| 10:00am – 12:30pm | Some go on with their local business, while some take their rest by sleeping Before they prepare lunch. |
| 12:30 – 2:00pm | they prepared lunch. and pray after noon prayer |
| :00 – 4:00pm | Tidy up the House, wash the plate and prepare their Children for evening religious school |
| 0 – 6:30 pm | prapare Dinner for the family, ~~prayer~~ pray ~~maagrib~~ magrif prayer |
| 30 – 9:00 | Have their Dinner, pray and family discussion |
| 00 – 10:30 | listen to news and then go to sleep |



KUNDIN SAMAR DA TSARIN CIGABAN CIKIN GARIN RANO 2016





## KADARORI

Kusan mafi akasari mazauna wannan gari suna da sana'oin da suka dogara da su, waɗanda suka haɗa da noma, kiwon shanu, Gidaje, ababan hawa da kuma kamfaninnika. Waɗansu kuma suna da ƙananan sana'oi kamar kantin sayar da kayan masrufi, kantin sayar da magunguna, wajen sayar da abincida dai sauransu.

















## ‘YANCIN ƊAN’ADAM

‘Yancin mata shi ne haƙƙoƙin da aka keɓe musamman domin mata da 'yanmata a kasashen duniya masu yawa. A wasu wuraren, ire-iren waɗannan haƙƙoƙin an tabbatar da su ta hanyar yi musu doka da tsarin zamantakewar Al'umma. A wasu wuraren kuwa, a iya cewa an yi watsi da su. Lamuran da ake dangantawa da haƙƙin mata ba a taƙaita su ga 'yancin yin zaɓe ko taƙaita haihuwa ba kaɗai.

A arewacin Najeriya, al'ada da addini suna ci gaba da taka muhimmiyar rawa a sha'anin 'yancin mata, an samu cigaba sosai a 'yancin mata musamman wajen faɗaɗa tattalin arzikinsu da samun damar yin ilimi da kuma yadda suke shiga a dama da su a al'amuran al'umma. Duk da wannan ci gaban da aka samu, har yanzu akwai ƙalubale wajen sanya su cikin al'amuran shugabancin da jin ta bakinsu yayin a ɗaukar wata matsaya kan wani al'amari da ba su muƙamai da kuma ba su damar bayar da irin tasu gudummawar a al'amuran al'umma.

A garin cikin garin Rano, ana ƙarfafawa mata gwuiwa domin su nemi ilimi kowane iri. Duk da haka akwai da yawansu sukan kasa ci gaba da karatu domin auren wuri da kuma wasu dalilai da suka haɗar da rashin kuɗi ko kuma waɗanda iyayensu suka rasu . Anyi amfani da wannan zane domin ya ƙara zurfafa fahimtar dangane da haƙƙin mata. Bugu da ƙari kuma zai taimaka man domin gano abubuwan da ke kawao cikas, yanayin da kuma matsyin mata a cikin al'umma.




Akwatin 'Yancin Mata Nacikin Garin Rano






AKWATIN 'YANCIN MATA NA CIKIN GARIN RANO

| Ɓangare | Sakamako (Mata) | Sakamako (Maza |
|---|---|---|
| Shugabanci | 1 | 1 |
| Samun Kuɗin Shiga | 2 | 3 |
| Kula da Gida | 2 | 1 |
| Mallakar Kadarori | 3 | 3 |
| Tsaro | 5 | 5 |
| Samun Damar Ilimi | 2 | 3 |
| Zartar da Hukunci Kan Al'amuran Al'umma | 1 | 1 |
| Sarrafa albarkatu | 5 | 5 |
| Shiga Al'amuran Al'umma | 1 | 1 |
| Aikin yi | 1 | 3 |

Wannan jadawali dake sama na kwatanta tazarar dake tsakanin maza da kuma mata yayin tantance haƙƙoƙin mata. Abin sha'awa shine akwai dangantaka mafi kusanci tsakani sakamakon kowannensu, wannan shike nuna cewa sun fahimaci banbancin da ke tsakanin maza da mata a wannan gari.

A wannan gari Rano, mata basa taka wata rawa dangane da har gudanar mulki amma suna shiga ana damawa dasu a harkoki na al'umma dai-dai misali. Mata nada ƙarfin iko a harkar gudanar tattalin arziƙi amma banda ta siyasa. An gamsu cewa mata nada damar samun ilimi amma suna taka rawa kaɗanne wajen tafida harkokin kula da gida. A wani ɓangaren kuma, mata ana basu cikakken 'yanci wajen basu kariya,wanda aka bashi mizanin lamba 5 daga duk ɓangarorin maza da mata. Haka kuma suna da cikakken haƙƙi wajen sarrafa kadarorin da suka mallaka.










Koda yake ba duk ne 'yancin mata da ake tauyewa ba, da yawansu an barshine saboda addini musulunci da kuma al' adu. Za a iya gani a akwati mai lamba 4, an bar wasu 'yancin mata. Duka mazan da matan sun bayyana mizanin 'yancin mafi ƙanƙancin lamba ɗaya.Waɗan su daga 'yancin matan da aka bai ya haɗar da; rashin shiga a dama dasu wajen shiga harkokin jama'a, Zartar da hukunci kan al'amuran al'umma samun matsayi na jagoranci. A wani ɓangaren kuma, mata ana basu cikakken 'yanci wajen basu kariya,wanda aka bashi mizanin lamba 5 daga duk ɓangarorin maza da mata. Haka kuma an a baiwamata damar samun ilimi, da ayyukan yi da kula da gida ambasu mizanin lamba biyu kowannen.


Idan ka haɗa jadawalin maza da na mata, za a iya ganin ɗan bambanci kaɗan wajen 'yancin samun kuɗin shiga dana mallakar kadarori da sarrafa albarkatun .Jadawalin mazan da mata an sanyashi cikin akwatin dake biye a ƙasa ajere.

AKWATIN 'YANCIN MATA NA CIKIN GARIN RANO

| ƁANGARE | SAKAMAKO (MATA) | SAKAMAKO (MAZA |
|---|---|---|
| Shugabanci | 2 | 2 |
| Kuɗin Shiga | 1 | 1 |
| | 3 | 5 |
| Kula Da Gida | 3 | 2 |
| Tsaro | 5 | 5 |
| Samun Damar Ilimi | 2 | 2 |
| Zartar Da Hukunci Kan Al'amuran Al'umma | 1 | 1 |
| Sarrafa Albarkatu | 3 | 4 |
| Mallakar Kadarori | 1 | 3 |
| Shiga Al'amuran Al'umma | 1 | 1 |




Ra'ayin Mata Kan Damarmaki




Ra'ayin Maza Akan Mata Kan Damarmaki



KUNDIN SAMAR DA TSARIN CIGABAN CIKIN GARIN RANO 2016




TAKE HAKKOKIN MATA

An lissafa haƙƙi ne domin a gano yadda ake tauye 'yancin jama'a cikin garin Rano. An hana al'ummar cikin garin Rano waɗannan haƙƙoƙin:

- Haƙƙin ingantattun ababen more rayuwa ( Lafiya)
- Haƙƙin ingantattun kayan more rayuwa ( Ruwan Sha)
- Haƙƙin ababen jin daɗin rayuwa ( Rashin aikin yi)
- Haƙƙin ababen more rayuwa ( Hanya)

Waɗannan haƙƙkoƙi da aka tauyewa mutanen wannan cikin garin Rano ya haifar da matsaloli da suka haɗa da harkar rashin ruwan sha, rashin aikin yi da kuma rashin ingantattun hanyoyi. Bugu da ƙari an tauye musu haƙƙin samun ingantacciyar lafiya saboda rashin samun mata ma'aikaciya a babban asibitin wannan gari.

Akwatin sama na nuna mizanin maza da mata yayin tantance haƙƙoƙin mata a cikin cikin garin Rano. Abin sha'awa shine, akwai kusanci soasi ra'ayoyin ɓangarorin, kamar yadda al'ummar cikin Garin Rano ta nuna awajen sanya mizani kuma sun fahimci harkokin haƙƙin jinsi.

A cikin garin Rano, mata basa taka wata rawar wajen harkokin al'ummar garin.Amman dai suna da kazar kazar a harkokin garin duk da dai ba a sanya su a ciki. Mata suna da ƙwazo sosai wajen ƙananan sana'oi amman banda na siyasa

TANTANCE MATSALOLI TA AMFANI DA BISHIYAR MATSALOLI

Bishiyar matsaloli ta taimaka wajen tantance manyan matsalolin da ke addabar garin. Bishiyar hoto ne da ke nuna dangantaka tsakanin abubuwan da suka haddasa matsalolin da kuma tasirinsu. Bishiyar matsaloli tana buɗe ƙofar shiga tsakani tun daga tushen abubuwan da suka janyo ta da zummar warwarewa. Gangar jikin matsalar, kamar yadda aka nuna,ƙarancin ruwan sha. Abubuwan dake jawo kamar yadda aka tattauna da mutanen garin sune kamar yadda ake ganinsu ajikin bishiyar a ƙasa:

| JIHAR | KANO | | | KARAMAR HUKUMA | RANO | | GARI | | RANO | |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|
| Rashin cancanta /cancanta a samu (mata, yara, talakan da ba shi da fili ko rukunin jama'ar da aka gano) | Adadin waxanda suka cancanci su samu a yankin da aka yi shirin | | Al'amari | Abubuwan da suka haddasa | Haƙƙoƙin da aka tauye | Kundin tsarin mulki/ policy entitle ment | Cikin Garin Rano Rashin cancanta/ cancanta a samu (mata, yara, talakan da ba shi da fili ko rukunin jama'ar da aka gano) | | Adadin waxanda suka cancanci su samu a yankin da aka yi shirin | Al'amari |
| | Maza | Mata | | | | | Maza | Mata | | |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 7,497 | 7,047 | Rashin kayan koyo da koyarwa da kwararrun malamai. | Karancin malamai da rshin aiwatar da manufofin da aka tsara | Haƙƙin samun Ingantaccen Ilimi | Kundin tsarin mulkin Najeriya | 7,497 | 7,047 | Ma'aikatar ruwa | ƙungiyoyi masu zaman kansu |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 7,497 | 11,452 | Karancin ma'aikatan lafiya da kayan aiki a cibiyoyin lafiya | Karancin ma'aikata da rshin aiwatar da manufofin da aka tsara | Haƙƙin samar da kiwan lafiya | Kundin tsarin mulkin Najeriya | 7,497 | 7,047 | Ma'aikatar ci gaban ƙananan hukumomi | ƙungiyoyi masu zaman kansu |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 7,497 | 11,452 | Rashin ingantancen ruwan sha | Rashin jagoranci na gari da cin hanci da rashawa | Haƙƙin samar da kayan aiki | Kundin tsarin mulkin Najeriya | 7,497 | 7,047 | Ma'aikatar lafiya | Kamfanonin ginegine Kungiyoyi masu zaman kansu |
| Maza, Mata da Matasa | 7,497 | 11,452 | Hanyoyi mararsa kyau | Rashin jagoranci na gari da cin hanci da r ashawa | Haƙƙin samun ingantattun kayayyakin more rayuwa | Kundin tsarin mulkin Najeriya | 7,497 | 7,047 | Ma'aikatar aiyuka Shugaban ma''aikata | Kungiyoyi masu zaman kansu LHC |

# KALUBALEN DA KE FUSKANTAR CIKIN GARIN RANO A HALIN YANZU

Mutanen Rano sun zayyana matsaloli shida waɗanda suka addabesu; rashin ingantaccen kayan koyarwa a makarantu da rashin ƙwararrun malamai, ƙarancin ingantaccen ruwan sha, rashin hanyoyi masu kyau, rashin aikin yi da shan miyagun ƙwayoyi. Waɗannan matsaloli an basu mataki ta hanyar sauƙi na zaɓe da aka kaɗa kamar yadda aka zayyana a akwati na 7.





Ambaiwa Ilimi mataki na farko, ƙarancin kayayyakin koyarwa da rashin ƙwararrun malamai da ƙarin makarantu. Matsalar ilimi itace babbar ƙalu bale a cikin garin Rano . Koda yake al'ummar cikin Garin Rano sunyi ittifaƙin idan har anyi maganin matsalar ilimi, to rashin aikin yi ma zai ragu, kuma shaye shayen ƙwayoyi zai zama tarihi.

Rashin ƙwararrun ma'aikatan lafiya awani ɓangaren da rashin kayan aiki yazo na biyu, magance wannan matsalar lafiya zai rage mace macen mata wajen haihuwa da ƙananan yara.

Bugu da ƙari wannan al'umma sun ƙara da cewar unguwar sabuwar cakwaya da kuma ta shagari kwatas na fuskantar matsalar zaizayar ƙasa.






Figure 1 Hoton Yana Nuna Yadda Al'ummar Cikin Gari Rano Suka Baiwa Matsaloli Mataki

Table: 1. Sassauƙar Hanyar Jera Matsaloli

| Lamba | Al'amari (Buƙatu) | MATA | YARA | MAZA | ADADI | MATSAYI |
|---|---|---|---|---|---|---|
| **1.** | Ilimi: ƙarancin kayayyakin koyarwa da rashin ƙwararrun malamai da ƙarin makarantu | 30 | 14 | 92 | 1,36S | 1ST |
| **2.** | Lafiya | 3 | 9 | 88 | 100 | 2ND |
| **3.** | Kyakkyawan ruwan sha | 0 | 14 | 24 | 38 | 4TH |
| **4.** | Hanyoyi mararsa kyau | 2 | 8 | 55 | 65 | 3RD |
| **5.** | Rashin aiki | 0 | 6 | 28 | 34 | 5TH |
| **6.** | Shaye shayen ƙwayoyi | 0 | 1 | 15 | 16 | 6TH |

## HOTUNAN DA KE BIYE, NA CIKIN GARI RANO YAYIN LOKACIN KAƊA KURI'A




| Issues | Women | Children | Men | Total | Rank |
|---|---|---|---|---|---|
| 1 Drainage | 0 9th | 0 | 6 9th | 06 | 9th |
| 2 Road | 20 3rd | 05 4th | 78 1st | 103 | 2nd |
| 3 Lack of portable water | 28 2nd | 15 3rd | 61 3rd | 104 | 1st |
| 4 Lack of Electricity | 10 5th | 0 | 52 4th | 62 | 5th |
| 5 Unemployment | 7th 07 | 0 | 74 2nd | 81 | 4th |
| 6 Education | 5th 10 | 33 2nd | 19 7th | 62 | 5th |
| 7 Health | 30 1st | 40 1st | 17 8th | 87 | 3rd |
| 8 PWD Empowerment | 7th 07 | 0 | 21 6th | 28 | 8th |
| 9 Drug Abuse | 19 4th | 0 | 24 5th | 43 | 7th |











Figure 2. Hoton Yana Nuna 'Yan Cikin Garin Rano Lokacin Kaɗa Kuri'a Domin Zaƙulo Mafi Buƙatar Matsala

# TANTANCE MATSALOLI TA AMFANI DA BISHIYAR MATSALOLI




Matsalolin da aka gano, an zurfafa tattaunawa da zaƙulo wadan da ake sa ran zasu kawo warakar matsalolin cikin garin Rano daga Kungiyoyi da mutanen da za su iya tallafawa. Su mutanen da ƙungiyoyin da 'yan Garo suka zaƙulo ana sa ransu kawo kyakkawan canjin game da matsalolin. Duba akwati na 8 dake biye.





Table 2. Kungiyoyi Da Mutanen Da Za Su Iya Tallafawa

| Abubuwan da aka Gano | Waɗanda za su Iya Tallafawa | Cibiyoyi | Manyan buƙatu/ zaburarwa domin kawo canji | Matakin ƙarfin ikon kawo canji |
|---|---|---|---|---|
| 1.Karancin ruwan sha<br>2.Hanya<br>3.Lafiya Rashin Aikin yi | 1.Sarkin Rano<br>2.Kansila<br>3.Chiyaman<br>4.A.A. Rano<br>5.Ɗanmajalisa ta Jiha<br>6.Ɗanmajalisar wakilai ta Tarayya.<br>7.Sarkin Yaƙin Rano<br>8.Chiyaman Shaka Super Market<br>9.Maáji Ali Rano<br>10.Sani Haruna | 1.Ma'aitatar Rauwa<br>2.Maáikatar ci gaban ƙananan Hukumomi<br>3.Cibiyar masarautar Rano<br>4.Ma'aikatar Lafiya<br>5.Gidauniyar A.A. Rano<br>6.Kungiyar cigaban Rano<br>7.Ma'aikatar yaɗa labarai<br>8.Cibiyar ci gaban matasa ta Kasa. | 1.Doncigaba<br>2.Siyasa<br>3.Siyasa<br>4.Don cigaba<br>5.Siyasa<br>6.Siyasa<br>7.Doncigaba<br>8.Donci gaba<br>9.Don cigaba<br>10.Don cigaba<br>11.Doncigaba | 1.M<br>2.M<br>3.H<br>4.H<br>5.H<br>6.M<br>7.M<br>8.M<br>9.M<br>10.M<br>M |
| | | | | |

Karin haske: H - Sama sosai, M- Tsaka-tsaki L-qasa

## WAƊANDA ZA SU IYA TALLAFAWA

Masu Karfin Iko

Bayan gano matsalar ruwa, hanya, lafiya da rashin aikin a matsayin manyan matsalolin dake damun cikin garin, al'umma sun kuma zaƙulo mutane, cibiyoyi da ma'aikatu da ake ganin zasu iya taimakawa wajen fitar da wannan gari daga cikin halin da ya sami kansa.


Daga cikin irin waɗanda al'ummar wannan gari suka gano domin taimakawa sun haɗarda masu hannu da shuni, maigari, shugaban ƙaramar hukuma ta Rano, kwamishinan ma'aikatar lafiya, Dan majalisa na jihar Kano, Dan majalisar wakilai ta tarayya a matsayin waɗanda ake ganin zasu iya tamakawa.

## CIBIYOYI

A ɓangare cibiyoyi kuwa, ma'aikatar ruwa, ma'aikatar ƙananan hukumomi, ma'aikatar yaɗa labarai, cibiyar ci gaban matasa ta ƙasa, Gidauniyar A.A. Rano ma'aiktar lafiya da kuma ƙungiyar cigan Rano.

## TANTANCE YANAYIN KARFIN IKO

An yi amfani da tsarin zane na Venn domin gudanar da wannan tantancewar. Haka kuma an yi amfani da tsarin zanen Venn domin tantance matakin ƙarfin ikon da wani mutum ko wasu ƙungiyoyi ke da shi da kuma alaƙarsu da juna.





Akwati Na 7.





Zanen ya fitar da mutane da cibiyoyi waɗanda suke da ikon warware al'amari ko matsalar da aka gano.



Wannan zane na sama na nuna mana irin mutane da kuma cibiyoyi da ake sa ran zasu iya warware mana matsaloli kamar haka : cibiyar ƙaramar hukuma da kuma majalisar jiha suna da matakin ƙarfin ɗaya, duk da haka ƙaramar hukuma itace ke tsakanin al'umma da kuma Ɗan majalisar jiha da kuma Ɗan majalisar tarayya.

Dagaci, Kansila , masu hannu da shuni da kuma shugaban ƙaramar hukuma suna da matskaicin ƙarfin iko wajen kawo canji ga al'umma. Masu unguwanni ma suna matsakaicin ƙarfin iko wajen kawo canji duk da cewar suna da dangantaka kai tsaye da Al'umma.

**Tantance abinda Haɗura ka iya Jawowa**

A vangaren tantance abinda...haxura da ka iya afkuwa, mutanen cikin garin Rano sun tattauna yanayin da zai iya kawo cutarwa, abinda zai kawosu da illolin su. Jinsin da yafi kowanne fuskantar yiwuwar gamuwa da illolin da kuma yadda zai iya kawo canji duk sun bayyana su a akwatin na 9.


Table 3. Tantance Haxura Da Ka Iya Afkuwa

| ABIN CUTARWA | ABINDA KE KAWOSU | ILLOLI | MIZANI | MATSAYIN FARUWAR SU | JINSIN DA YAFI CUTARWA |
|---|---|---|---|---|---|
| Shan miyagun ƙwayoyi<br><br>Fashi da makami | 1.Rashin Aikin yi<br>2.Rashin ci Gaba da Karatu<br>3.Rashin yin aikin da ya kamata daga hukumomin tsaro | 1.Na jawo taɓuwar Hankali<br>2.Theft<br>3.Rashin Tarbiyya<br>4.Na cutar da matasa | Sama | Yana ƙaruwa | Matasa maza<br><br>Matasa mata |
| | 1.Rashin aikin yi<br>2.Shan miyagun ƙwayoyi<br>3.Rashin kyakkawar tarbiyya daga iyaye da kuma Al'umar gari | 1.Na ƙara haɓaka rashin tarbiyya<br>2.Na jawo rasa rayuka da dukiyoyi<br>3.Rashin tarbiyya | Kasa | Yana Raguwa | Matasa maza |





Shan miyagun ƙwayoyi na daga cikin manyan matsaloli dake addabar wannan al'umma , wannan ya kasan ce ne saboda rashin aikin yi, rasin ci gaba da karatu, rashin aikin da yay a kamata ayi daga cibiyoyin tsaro da kuma rashin ingantatciyara manhaja ta ilimi daga ɓangaran gwamnati . sakamakon haka yak an kai ga samun taɓuwar hankali, sace-sace da kuma ya na ɓata matasa wanda ya na ƙara kawo rashin ci gaba a cikin al'umma. Wannan abu ne da ke faruwa koda yaushe da kuma shekara shekara ya yin da ake wasu bukukuwa . Fashi da makami ma nada daga cikin matsalolin dake damun wannan gari wanda yana faruwa ne saboda rashin aikin yi da kuma shan miyagun ƙwayoyi da ƙarin rashin tarbiyya wanda shima kan jawo asarar rayuka da kuma dukiyoyi . al'ummar wa gari sun baiwa shan miyagun ƙwayoyi a matsayin matsala ta farko dake damunsu kuma tafi damunsu saboda itace kullun take ta faruwa kuma take da wahalar magancewa, yayi n da kuma fashi da makami ya zo mataki na biyu saboda al'umma tare da taimakon ƙungiyoyin tsaro na sa kai suna ƙoƙarin magance ta .




TANTANCE HANYOYIN SAMUN BAYANAI

Manyan hanyoyin samun bayanai a cikin garin Rano sun haɗa da radiyo da talabijin da yanar gizo da jaridu da mujallu da tauraron Ɗan'Adam da shela da wayar tafi-da-gidanka da tattaunawa da kuma tarurruka. A wasu lokutan akan yaɗa bayanai a wuraren raɗin suna ko ɗaurin aure da kuma cibiyoyin addini da ke garin.

Wayar tarho da tattaunawa fuska da fuska hanyoyi ne da al'ummar cikin garin Rano suke isar da saƙonni ga takwarorinsu nawasu unguwannin. Dagaci da masu unguwanni sune masu magana da yawun al'umman garin, kuma suna da ƙarfin iko fiye da kansilan da aka zaɓa.

Akwati Na 8








# TSARINDA ZA A BI

A ƙarshen tattaunawar, an fitar da ƙwaƙƙwaran tsarin da za a bi domin warware matsalolin da aka gano ta hanyar yin amfani da gudummawar kowa da kowa da wasu dabaru domin tantance abubuwan da ke ciwa al'ummar cikin garin Rano tuwo a ƙwarya. Abin da ke biye tsarine na ayyukan da za aiwatar domin ganin mafarkin garin ya zama gaskiya

## Akwati Na 4 Tsarin Da Za'a Bi Na Ci Gaban Cikin Gari Rano

| Muhimman Abubuwa | Hanyar da aka Tsara | Masu yin Aiki | Abubuwan da ake Buƙata | Lokaci | Matsaloli | Hujjar Samun Nasara |
|---|---|---|---|---|---|---|
| Ziyartar wasu rukunonin Al'umma a cikin Garin Rano | Ziyara ta kai tsaye | Kwamitn rubuta kundin ci gaban cikin garin Rano | •Bayanin shirin<br>•Taswirar rukunonin Al'umma | Sati biyu 22 Nuwamba 2015 | Abin hawa kuɗi domin sadar wa | Rahoto |
| Rubutaccen bayani game da kundin | Gabatarwa da karɓar Shawarwari | CITAD da al'ummar garin | Mutanen da zasu haɗa Rahoto | Janairu 2016 30 ga Oktoba 2015 | Lokaci | Cikakken rubutaccen bayani game da kundin. |
| Kaddamarwa da kundin ci gaban cikin Gari Rano | •Gayyata<br>•Hadin gwuiwa da 'yan jarida<br>•Taron tsare-tsare | CITAD da al'ummar garin | Mutane Yanjaridu Takaddar gayyata 'Yan jarida | $30^{th}$ ga Yuni 2016 | Lokaci Kuɗin Zirga zirga | Ranar Kaddamarwa da kundin cikin garin Rano |
| Ziyarar ƙarfafa gwiwa ga waɗanda nauyi ya hau kansu | Ziyarce-ziyarce | CITAD da al'ummar garin | Kundin ci gaban garin Rano 'Yanjarida abin hawa | Mutanen Garin<br><br>Manema Labarai | Lokaci | Rahoton Kwamiti |